# Rayuwar Imam

<"xml encoding="UTF-8?>

Rayuwar Imam Mahadi

Don Allah a yi mana bayanin rayuwar Imam Mahadi (a.s) tun farko a lokacin mahaifinsa? Kuma shin akwai karamomi da ya nuna tun yana karami?

Wannan zamanin yana da muhimman abubuwan da zamu yi nuni da su a nan: Bayan haihuwar Imami na sha biyu abin da ya biyo baya shi ne tsoron kada Shi'a su sami kuskure wajan sanin Imami na karshe, su kuma fada cikin halaka. Sai Imam Askari (a.s) ya dauki nauyin sanar da Imam Mahadi (a.s) ga manyna mabiyansa da sahabbansa domin su ma su isar da sakon haihuwarsa ga sauran mabiya Ahlul Baiti (a.s), don haka ne ma akwai kuma tsoron kada Imami na karshe ya sami barazana.
Ahmad dan Ishak yana cewa: Na tafi domin hidima ga Imam Askari (a.s), kuma ina son in tambaye shi game da Imami bayansa, amma kafin in yi magana sai ya ce: Ya Ahmad! Haka ne cewa tun ranar da Ubangiji madaukaki ya halicci Annabi Adam (a.s) bai taba barin Duniya haka nan ba hujjarsa ba kuma har zuwa ranar kiyama ba zai yi ba! Ta hannun hujjarsa ne ake dauke bala'i daga mutanen Duniya, kuma da albarkarsa ne ake ruwan sama kuma arziki yake futowa daga kasa. Sai na ce ya dan Manzon Allah (a.s) wane ne mai maye gurbinka? Sai ya gaggauta zuwa cikin gida a lokacin akwai wani yaro dan shekara shida kamar wata mai haske yana dauke da shi a kafadarsa, sai ya ce: Ahmad dan Ishak! Ba don ka kasance abin so wajan Allah da hujjojinsa ba, da ban nuna maka wannan yaron nawa ba! Yana da suna da alkunya irin ta Manzo (s.a.w), kuma shi ne wanda zai cika Duniya da adalci bayan an cika ta da zalunci. Sai na ce: ya dan Manzon Allah! Shin akwai wata alama da zuciyata zata samu nutsuwa da hakan?! Sai wannan yaron ya bude baki da harshen larabci mai fasaha ya ce: "Ni ne ragowar hujjar Allah a bayan kasa! mai daukar fansa a kan makiyansa" .
Kuma Muhammad dan Usman da wasu daga manyan Shi'a suka rawaito wasu labarai masu kama da hakan. Kamar ruwayar ta zuwan mutum arba'in wajan Imam Askari suka tambaye shi game da halifansa bayansa sai ya gaya musu cewa: "bayana wannan shi ne imaminku kuma halifana…".

Muhammad dan Ibrahim yana cewa: Imam Hasan Askari (a.s) ya yanka tumaki ga shi'arsa sannan sai ya ce da su: "Wannan akikar sunan dana Muhammad ne" .

An samu karamomi da yawa da suka faru a lokacin farkon rayuwar Imam Mahadi (a.s) kafın lokacin buyansa, wadannan karamomi an gafala ga barinsu amma zamu kawo misali daga gresu:

Ahmad dan Ibrahim Naishaburi yana cewa: A lokacin da Amru dan Aufu ya so kashe ni, na tsorata kwarai da gaske, don haka sai na yi bankwana da iyalina na tafı gidan Imam Askari (a.s) domin in yi bankwana da shi. Da na shiga gidan Imam Hasan Askari (a.s) sai na ga wani yaro kamar wata yana mai haske da na dimauce saboda hasken fuskarsa, na kusance shi har na manta da abin da yake cikn raina na tsoron mutuwa. Sai yaron nan ya ce da ni: "Ya Ibrahim babu bukatar ka koka kan haka, da gaggawa Allah zai kare ka daga sharrinsa. Sai na sake dimauta, na ce da Imam Askari: Wannan wane yaro ne? Sai ya ce: Wannan dana ne kuma mai maye gurbina. Ibrahim ya ce: Sai na fito waje a lokacin ina mai dogara da nutsuwa da abin da na ji daga Imami na goma sha biyu (a.s), bayan dan lokaci ammina ya ba ni labarin albishir da cewa an kashe Amru Dan Auf .

Imam Mahadi (a.s) ya sha ba wa shi'arsa amsa mai gamsarwa game da mas'aloli daban-daban, yana mai sanya nutsuwa a zukatansu, ga wata ruwaya a takaice game da hakan:
Sa'adu dan Abdullah kummi daga manyan Shi'a tare da Ahmad dan Ishak kummi wakilin Imam Hasan Askari sun tafı wajansa da wasu tambayoyi domin neman amsarsu, yana fada game da wannan haduwar cewa: Na so in yi tambaya sai Imam Askari (a.s) ya nuna dansa (a.s) ya ce: Ka tambayi hasken idanuna (a.s), sai wani yaro ya kalle ni ya ce: "Ka tambayi duk abin da kake so"… sai na tambayi ma'anar (K.H.Y.A'.S.)? Sai yaron (a.s) ya ce da ni; wannan labarin gaibi ne da Allah ya ba wa bawansa Zakariyya (a.s) ya kuma sake bayar da shi ga Muhammad (s.a.w). Lamarin shi ne: Annabi Zakariyya (a.s) ya roki Allah ya sanar da shi sunayen biyar daga bayinsa mafı daukaka (a.s) sai Allah ya aiko Jibril ya sanar da shi. Duk sa'adda Zakariyya ya ambaci sunan Muhammad (s.a.w) da Ali (a.s) da Fadima (a.s) da Hasan (a.s) sai duk matsalarsa ta kau bakin cikinsa ya dauke, amma da ya ambaci Imam Husain (a.s) sai makogwaronsa ya rike da bakin ciki. Wata rana sai ya ce: Mene ne ya sanya idan na ambaci sunan hudu na farko sai bakin ciki da damuwata su tafı, zuciyata ta nutsu, amma idan na ambaci Husain (a.s) sai hawaye su zubo mini, sautin kukana ya daukaka?! sai Ubangiji ya sanar da shi labarin Imam Husaini (a.s). ya ce da shi: (K.H.Y.A'.S.).

K- Tana nufın Karbala;
H- Tana nufın kashe shi da shi da zuriyarsa;
Y- Tanan nufın Yazid Wanda zai kashe Husain (a.s)
A'- Tana nufın kishirwarsa;
S- Tana nufın hakurinsa da juriyarsa da dagewarsa;

Sai na ce ya shugabana! Mene ne ya sanya aka hana mutane su zabi shugaba da kansu? Sai ya ce: Shugaba mai gyara ne ko mai barna? Sai na ce mai gyara ne. Sai ya ce: Saboda cewa ba wanda ya san abin da yake cikin zuciyar wani cewa yana tunanin gyara ne ko kuma barna, shin babu tsammanin mutane su zabi mai barna? Sai na ce: Haka ne. Sai ya ce: Wannan shi ne dalilin .

Daga cikin ayyukan Shi'a akwai bayar da kyauta da fıtar da hakkin dukiyoyinsu na wajibi da aika su zuwa ga imamai (a.s), kuma da wadannan dukiyoyi ne imamai (a.s) suke kawar da matsaloli da kuma daukar nauyin bukatun al'umma. Ruwayoyi da dama sun zo game da kai irin wadannan dukiyoyi zuwa ga Imam Hasan Askari (a.s) da kuma yadda Imam Mahadi (a.s) yana karamin yaro ya ware dukiyar haram daga cikin irin wannan dukiyoyi kuma ya ayyana masu su, da kuma masu su na asali, kuma ya yi umarni da a mayar da ita ga ma'abotanta na asali. Wanda yake neman karin bayani sosai game da irin wadannan ruwayoyi ya koma zuwa ga littafın Kamaluddin, juz'i na 2, hadisi 21, shafı 190 .

Imam Mahadi (a.s) ya kasance yana kebewa daga mutane kafın farawar boyuwarsa a karshen rayuwar babansa Imam Hasan Askari (a.s), bayan wafatin babansa shi ne ya yi mahaifın nasa sallar janaza. Akwai ruwaya mai tsayi game da wannan al'amari da Abul Adyan mai hidima ga Imam Hasan Askari (a.s) ya ruwaito, wanda yake son karin bayani ya koma zuwa ga littafın: Kamaluddin, hadisi 25, shafı 223 .

Hafız Muhammad Sa'id
hfazah@yahoo.com
Haidar Center for Islamic Propagation